# FADAKARWA

## A kan: Sanin makamar kasuwanci

## <u>Kashi na 3c:</u> Hanyoyin adana bayanai a kan kayan sayarwa

1. Kayan sayarwa a nan na nufin dukkan kayan da a ka sayo domin a sayar. Wadannan sune kayan da a ka ajiye a suto ko aka kasa a kanti domin jama'a su gain, su saya. Misali, mai sayar da kayan noma zai kasa samfurin takin zamani kala-kala, magungunan kwari, injinan feshi da sauransu.

2. Ya wajaba a adana bayanan kayan da ke kanti, sabo da yin haka ne zai sa a fahimci kayan da a ka sayar, wadanda aka sayo ko a ka yi oda. Wannan kuma zai taimaka a yi kyakkyawan tsarin yadda ya kamata a sayo ko ayin odar kaya ta yadda a ko da yaushe kaya ba za su yanke ba kuma ba. Kuma zai taimaka wajen hana karo irin kayan da ba a sayar ba.

3. Ana rubuta bayanin ko wanne kaya da ke kanti daki-daki.  ko wanne kaya a tantance masa nasa da ban.  Misali, idan za a adana bayani a kan maganin Gamalin dake kanti, za a yi sau biyu kullum a farko da karshen kowace ranar ciniki. wato budewa da rufewar kanti kamar haka:
   - Ranar da a ka sayo kaya
   - Ranar da kaya za su daina amfani
   - Daga inda a ka sayo
   - Adadin kayan da a ka sayo
   - Adadin kayan da a ka sayar
   - Adadin kayan da ya rage

| **Stock on Ultracide 1 liter bottles** | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|
| **Date** | **Opening stock including expiration date** | **Quantity sold** | **Quantity purchased** | **Supplier** | **Closing stock including expiration date** |
| 09 Jan 2009 | Feb 2010: 10<br>May 2010: 38 | 6 | | | Feb 2010: 4<br>May 2010: 38 |

| | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|
| 10 Jan 2009 | Feb 2010: 4<br>May 2010: 38 | 1 | | | Feb 2010: 3<br>May 2010: 38 |
| 11 Jan 2009 | Feb 2010: 3<br>May 2010: 38 | | 50 | Golden inputs | Feb 2010: 3<br>May 2010: 38<br>Dec 2010: 50 |
| 14 Jan 2009 | Feb 2010: 3<br>May 2010: 38<br>Dec 2010: 50 | 4 | | | May 2010: 37<br>Dec 2010: 50 |
| | | | | | |

**A yi hattara**

Kada a makara wajen sayar da kaya, watau, a guji barin kaya su wuce lokacin ka'idar amfaninsu ba a sayar ba. A tuna cewar ba za a iya ajiye kayan aikin gona dundundun ba. Wasu daga irin wadannan kaya ba sa wuce shekara guda basu lalace ba. Idan kuwa kaya suka wuce lokacin amfaninsu, to, bai kamata a sayar da su ba.

Hanyar da za a iya kauracewa wannan matsala ta dadewar kaya a hannu shine a fara sayar da kayan da suka fara shigowa kanti. Watau kada a fara sayar da sabuwar oda sai tsohuwa ta kare.

Sabo da haka yana da kyau masu sayar da kayan noma su fara sayar da kayan da ranar daina aikinsu tafi kusa. Misali idan dan kasuwa yana da katan uku na maganin ciyawa, kowanne mai ranar daina aiki dabam, kamar haka: Febrairu, 2009, Febrairu, 2010 da kuma Yuni, 2010; to ya kamata ya mayar da hankalinsa wajen sayar da wanda zai daina aikin Febrairu, 2009 kafin ya sayar da ragowar.